(١)

## ZAMAN LAFIYA TARE DA RAI DA SAURAN HALITTUN ALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Allah yana kiranku zuwa gidan zaman lafiya da aminci, yana kuma shiryatar da wanda yake so zuwa ga hanya madaidaiciya)** [Yunus: 25]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai zaman lafiya ɗabi'a ce mai girma ta mutuntaka, addininmu mai daraja ya kula matuƙa wajen kafa ta, addininmu addini ne na zaman lafiya da aminci, haka ma Annabinmu Annabi ne na zaman lafiya da aminci, gaisuwar da muke yi da juna a wannan duniyar, take ne na zaman lafiya da aminci, aljanna ma gida ne na zaman lafiya da aminci, gaisuwar da take tsakanin 'yan aljanna zaman lafiya ne da aminci, gaisuwar mala'iku ma zaman lafiya ne da aminci, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku zama masu son zaman lafiya tsakaninku da juna baki ɗaya, kada ku tayar da ƙabilancin zamanin jahiliyya da makamantan haka, na abubuwan da suke zama sanadiyyar rikici, da saɓani a tsakaninku, kada ku bi hanyar shaiɗan wanda take tunkuɗa ku zuwa ga**

**rabuwar kawuna, lallai shi shaiɗan maƙiyinku ne mai kuma bayyanar da gaba)** [al- Baƙra: 208], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Suna da gidan zaman lafiya da aminci a wurin Ubangijinsu..)** [al- An'am: 127], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Gaisuwarsu alama ce ta zaman lafiya da aminci..)** [Yunus: 10], Allah mabuwayin Sarki yana cewa: **(Da mala'iku da suke shigo masu ta dukan ƙofofi, suna ce masu: zaman lafiya da aminci sun tabbata a gare ku sakamakon haƙurin da kuka yi, kai madalla da wannan gida a matsayin sakamakon ƙarshe)** [ar- Ra'ad: 23 -24].

Saboda girma da darajar zaman lafiya da aminci ne Allah Ubangijinmu mai girma da buwaya ya kira kansa da sunan *"Assalamu"*, yana cewa: **(Shi ne Allah wanda babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, ainihin mamallakin komai, cikakken da babu wata tawaya tare da shi, kuɓutacce ga barin abin da bai dace da shi ba, amintacce ga barin naƙasa, wanda ya gasgata manzanninsa ta hanyar ƙarfafa su da mu'ujizozi, mai lura da komai, mai rinjayen da babu abin zai gajiyar da shi, mai babban sha'ani a ƙarfi da iko, wanda ya girmi duk wani abu da bai yi daidai da baiwarsa da hanawarsa ba, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya tsarkaka ga barin abin da suke haɗa shi da shi wajen bauta)** [al- Hashri: 23], Annabinmu mai tsira da aminci a koda yaushe ya gama sallah yakan yi addu'a, ya ce: **(Ya Allah kai ne Assalamu, duk wani zaman lafiya da aminci daga gare suke, lallai ya mai girma da karamci ka kai matuƙa wajen ɗaukaka)**.

Lallai zaman lafiya da aminci a Musulunci, zaman lafiya da aminci ne da suka game komai, Musulmi na haƙiƙa shi ne wanda ya zauna da kansa lafiya cikin rangwame, a koda yaushe kuma yake cikin zaman lafiya da aminci na haƙiƙa tare da iyalansa, da makusantansa, da maƙwabtansa, da abokansa, da sauran mutane baki ɗaya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa da hannuwansa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba.. Sai aka ce: wane, ya Manzon Allah? Sai ya ce: wanda maƙwabcinsa bai aminta daga cutarwarsa ba),** lokacin da aka tambaye shi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) game da wata mata, mai yawan azumi, da ƙiyamullaili, amma kuma tana cutar da maƙwabtanta da harshenta? (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) cewa ya yi: **(Ba ta da wani alhairi, 'yar wuta ce ita).**

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa babu yanda za a yi a samar da wannan zaman lafiyar, sai zukata sun tsarkaka, yana zama akwai wasu ƙa'idoji na imani, da na mutuntaka masu girma da suke yi masu jagoranci, a cikin muhimman waɗannan ƙa'idoji, dole ne mutum ya zama yana da fuska ɗaya, ta yanda zahirinsa zai yi daidai da baɗininsa, ba wai ya zama mai baki- ganga, da yake fuskantar waɗannan da wata fuska ta daban, da zai fuskanci saura ba, Annabinmu

(SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(A cikin mutanen da suka fi sharri akwai: mai fuska biyu, ya zo wurin waɗannan da wata fuska, ya tafi wurin waɗancan kuma da wata fuskar ta daban)**.

Haka ma a cikin muhimman ƙa'idojin akwai: mutum ya zama mai so ma mutane gaba ɗayansu alhairi, mai tausayi da sauƙin kai, da kuma ƙaunar mutane, mai haɗa zumunci, wanda mutane suke jin daɗin mu'amala da shi, da taruwa a gabansa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Imanin kowanne daga cikinku ba zai cika ba, har sai ya zama yana son ma ɗan uwansa abin da yake so ma kansa)**, ya kuma zama mabuɗin alhairi, makullin sharri, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin mutane akwai waɗanda suke a matsayin mabuɗai ne na alhairi, kuma makullai ne na sharri, haka ma a cikin mutane akwai waɗanda suke a matsayin mabuɗai ne na sharri, kuma makullai ne na alhairi, madalla da bawan da Allah ya sanya ya zama mabuɗin alhairi, makullin sharri.. Bone ya tabbata ga bawan da Allah ya sanya makullin alhairi, mabuɗin sharri a hannunsa)**.

Haka ma a cikin muhimman ƙa'idojin akwai: mutum ya zama ya yi imani da haƙƙoƙin waninsa, na su rayu rayuwa mai cike da karama, da aminci, gami da kwanciyar hankali, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya halicci mutane ne a matsayinsu na mabambanta, Allah yana cewa: **(Da Ubangijinka ya ga dama, da ɗaukacin waɗanda suke a doron ƙasa sun yi imani, shin**

**tursasa mutane za ka yi har sai sun zamo muminai?)** [Yunus: 99], ya kuma yi imani da cewa akwai wasu ƙa'idoji na mutuntaka da suka haɗe ɗaukacin bil'adama, kuma dukan Shari'o'in Allah sun haɗu akansu, yin riƙo da su yana kai wa zuwa ga samar da natsuwa, da kwanciyar hankali, da zaman lafiya tsakanin mutum da zuciyarsa, da tsakaninsa da sauran al'umma baki ɗaya.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai Musulmi na haƙiƙa yana rayuwa ne cikin zaman lafiya da aminci tare da dukan halittun Allah, ba ya cutar da koda dabba ce, ba ya ƙona tsirrai, ba ya sare bishiyoyi, balle 'ya'ya masu amfani da suka fitar, shi a koda yaushe ginawa yake yi, bayarwa yake yi, yana son alhairi ba ya son sharri, gini yake yi ba ya rusawa, rayawa yake yi ba ya lalatawa, ba ya yin ɓarna a bayan ƙasa, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) shi ne ya kafa wannan tushe na zaman lafiya tare da sauran halittun Allah, lallai shi ɗin (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana nan a matsayinsa na rahama da jinƙai ga ɗaukacin halitta, kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **(Ba mu aiko ka**

**ba, sai domin ka zama rahama da jinƙai ga talikai)** [al-Anbiya: 107]. Kaman yanda za mu ga haka a fili lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya shiga gonar wani mutum daga cikin *"al-Ansar"*, sai ga wani raƙumi, lokacin da raƙumin ya ga Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) sai ya tafi wurinsa yana hawaye, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya zo, ya shafi kansa, sai ya yi shiru, sai ya ce: **(Wane ne mai wannan raƙumi, na wane ne wannan raƙumi?)** sai wani matashi daga cikin *"al- Ansar"* ya zo ya ce: Nawa ne ya Manzon Allah, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ashe bai kamata ka ji tsoron Allah game da al'amarin wannan dabbar da Allah ya mallaka maka ba? ya kawo ƙarar cewa kana barinsa da yunwa, kana kuma wahalar da shi da aikin mai yawa)**.

lallai babu abu mafi kyau da ya kai a ce mutum yana rayuwar zaman lafiya da aminci tare da zuciyarsa, yana rayuwar zaman lafiya da aminci tare da iyalansa, yana kuma rayuwar zaman lafiya da aminci tare da maƙwantansa, yana rayuwar zaman lafiya da aminci tare da abokan aikinsa, yana rayuwar zaman lafiya da aminci tare da kowa da kowa, yana rayuwar zaman lafiya da aminci tare da tare da dukan halittun Allah.

**Ya Allah Ubangiji ka sanya mu zama cikin ma'abota zaman lafiya da aminci, ka kuma sanya mu a gidan zaman lafiya da aminci albarkacin rahama da jinƙanka.**